"Za ku neme ni ku same ni, idan kun neme ni da zuciya ɗaya."

# YADDA ZA A SAN ALLAH

## YADDA ZA A SAN ALLAH

Kamar Annabi Ibrahim "aminin Allah" ne saboda yardarsa da biyayyarsa ga Allah, kai kuma ka iya fara sanin Allah, ka sami jinƙansa, da salamarsa, da albarkarsa. Sanin Allah ta wurin yarda da shi, wato ba da kanka gare shi sosai ta wurin bangaskiya, shi ne abu mafi girma, mafi amfani da mutum zai yi muddin ransa. Abin al'ajabi ne yadda Allah yake bayyana kansa ga dukkan waɗanda ke nemansa da zuciya ɗaya.

Idan ka juya daga taka hanya, ka kuma yarda sosai ga Allah, Ruhunsa Mai Tsarki zai kasance a cikinka. Ba abin da zai iya raba ka da ƙaunarsa lokacin da kake dogara ga alkawaransa kana binsa game da biyayya. Shi zai kasance Allahnka, kai kuma ka zama abin tamani gare shi. Za ka gane yadda ya saye ka da babban tamani, yana kuma neman zumunta da kai—yanzu da kuma har abada.

Sai ka roƙi Allah ya ba ka ganewa lokacin da kake nazarin ayoyin nan daga Maganar Allah. Allah dai yā hura wa bayinsa maganan nan suka kuma rubuta ta ta wurin ikonsa.

A ɗan littafin nan an ɗauki nassoshi duka daga Littafi Mai Tsarki: Shi ne Attaura, da Zabura, da rubutun annabawa, da Linjila.

## BA WANI ALLAH MAI GASKIYA SAI ALLAH 1

"Ubangiji shi ne Allahnmu, Ubangiji ɗaya ne. Sai ku ƙaunaci Ubangiji Allahnku da zuciya ɗaya, da dukan ranku, da dukan ƙarfinku."
—Maimaitawar Shari'a 6. 4b, 5

Ubangiji ne ya halicci sammai, shi ne wanda yake Allah! Shi ne ya shata duniya ya kuma yi ta, ya kafa ta, ta kahu da ƙarfi, za ta yi ƙarƙo! Bai halicce ta hamada da ba kome a ciki ba, amma wurin zaman mutane. Shi ne wanda ya ce, "Ni ne Ubangiji, ba kuwa wani Allah, sai ni." —Ishaya 45.18

Domin dukan al'umman duniya su sani Ubangiji shi kaɗai ne Allah, banda shi, ba wani."
—1 Sarakuna 8.60

"Ni kaɗai ne Ubangiji Allahnka. Ba wani allahn da zai sami ɗaukakata, ba zan bar gumaka su sami yabona ba." —Ishaya 42.8

"Ku ne shaiduna, . . . domin ku san ni, ku gaskata ni, ku kuma fahimta, ni kaɗai ne Allah. In banda ni ba wani Allah, ba a taɓa yin wani ba, ba kuwa za a yi ba. "Ni kaɗai ne Ubangiji, ni kaɗai ne wanda yake da ikon yin ceto."
—Ishaya 43.10b, 11

"Ku juyo wurina a cece ku, ku mutane ko'ina a duniya! Ni kaɗai ne Allah da ke akwai."
—Ishaya 45.22

## 2 ALLAH MAI JINKAI NE, MAI ALHERI KUMA

Ubangiji mai jinƙai ne, mai ƙauna ne kuma, mai jinƙirin fushi ne, cike yake da madawwamiyar ƙauna. Kamar yadda nisan sararin sama ke bisa kan duniya, haka kuma girman ƙaunarsa yake ga waɗanda ke tsoronsa.
—Zabura 103.8, 11

Amma ƙaunar Ubangiji ga waɗanda ke girmama shi har abada ce, . . . Waɗanda ke biyayya da umarnansa da aminci.
—Zabura 103.17a, 18b

Akwai wani Allah kamarka, mai yafe mugunta, . . . gama shi mai alheri ne. —Mika 7.18

"Ƙaunar Ubangiji ba ta ƙarewa, haka kuma jiyejiyanƙansa ba su ƙarewa." —Makoki 3.22

Ko da ya sa ɓacin rai, zai ji tausayi kuma, saboda tabbatacciyar ƙaunarsa mai yawa. —Makoki 3.32

Kai, ya Ubangiji, mai aminci ne ga masu aminci. —Zabura 18.25a

Ku yi godiya ga Ubangiji, gama shi nagari ne, ƙaunarsa madawwamiya ce! —1 Tarihi 16.34

"Na sani kai mai taushin hali ne, mai jinƙai, mai haƙuri. Kai kullum mai alheri ne, a shirye kake kuma." —Yunusa 4.2b

Daga zamanai har dai zuwa wani zamani, jinƙansa yana ga waɗanda ke tsoronsa. —Luka 1.50

## ALLAH YANA KAUNARKA 3

Ubangiji ya bayyana gare ni tun daga nesa cewa, ". . . Na kusace ki da madawwamiyar ƙaunata, ba zan fasa amintacciyar ƙaunata a gare ki ba." —Irmiya 31.3

Gama na san irin shirin da na yi muku, ni Ubangiji na faɗa. Shirin alheri, ba na mugunta ba. Zan ba ku gabata da sa zuciya.
—Irmiya 29.11

Ubangiji ya ce, "Ina ƙaunarku." —Malakai 1.2a

Kamar yadda uba yake yi wa 'ya'yansa alheri, hakanan kuwa Ubangiji yake yi wa masu tsoronsa alheri. —Zabura 103.13

Ɓacin zuciyata zai juya ya zama salama. (Ya Allah) ka ceci raina daga dukan hatsari, ka gafarta dukan zunubaina. —Ishaya 38.17

Mun sani, mun kuma gaskata ƙaunar da Allah ke yi mana. Muna ƙauna, domin shi ne ya fara ƙaunarmu. —1 Yahaya 4.16a, 19

"Ubangiji Allahnki yana tsakiyarki, mayaƙi mai cin nasara ne. Zai yi murna, ya yi farin ciki da ke. Zai sabunta ki da ƙaunarsa. Zai kuma yi murna da ke ta wurin raira waƙa da ƙarfi."
—Zafaniya 3.17

Ina misalin darajar madawwamiyar ƙaunarka, ya Ubangiji! Mutane sukan sami mafaka a ƙarƙashin fikafikanka. —Zabura 36.7

## MUHIMMIN ABU SHI NE SANIN ALLAH

"Amma waɗanda suka san Allahnsu za su tsaya da ƙarfi su yi wani abu." —Daniyel 11.32b

"Amma bari wanda zai yi fariya, ya yi fariya a kan cewa ya fahimce ni, ya kuma san ni. Ni ne Ubangiji mai yin alheri, da gaskiya, da adalci a duniya, gama ina murna da waɗannan abubuwa, ni Ubangiji na faɗa." —Irmiya 9.24

Masu farin ciki ne waɗanda suke bin umarnansa, waɗanda suke yi masa biyayya da zuciya ɗaya. —Zabura 119.2

"Na sa rai da mutuwa a gabanku, da albarka da la'ana. Ku zaɓi rai fa, don ku rayu, ku da zuriyarku. Ku ƙaunaci Ubangiji Allahnku, ku yi biyayya da maganarsa, ku manne masa, gama wannan shi ne ranku." —Maimaitawar Shari'a 30.19b, 20a

Gama ƙauna nake so, ba sadaka ba, sanin Allah kuma fiye da hadayu na ƙonawa. —Yusha'u 6.6

Kamar yadda kishimi yake marmarin ruwan sanyi daga rafi, haka nake marmarinka, ya Allah. —Zabura 42.1

Ubangiji kuwa ya ce, "Zan tafi tare da kai, zan kuma hutashe ka." —Fitowa 33.14

Ya ce, "Ku yi shiru, ku sani ni ne Allah." —Zabura 46.10a

## ZAMAN MUTUM BA TARE DA ALLAH BA ZAI KAI SHI GA MUTUWA



"Ubangiji yana tare da ku idan kuna tare da shi. Idan kuwa kun neme shi, za ku same shi, amma idan kun rabu da shi, shi ma zai rabu da ku." —2 Tarihi 15.2b

"Zuciya ta fi kome rikici, cuta gare ta matuƙa, wa zai san kanta?" —Irmiya 17.9

Hanyar da kake tsammani ita ce daidai, za ta kai ka ga halaka. —Karin Magana 16.25

Da ya ke Allah bai rangwanta wa mala'iku ba sa'ad da suka yi zunubi, sai ya jefa su Gidan Wuta, ya tura su cikin ramummuka masu zurfi, masu baƙin duhu, a tsare su har ya zuwa ranar hukunci. Ashe kuwa, Ubangiji ya san yadda zai kuɓutar da masu tsoronsa daga gwaje-gwaje, ya kuma tsare marasa adalci a kan jiran hukunci, har ya zuwa ranar shari'a. —2 Bitrus 2.4, 9

Amma idan kun ƙi yin biyayya da maganar Ubangiji, kuka kuma karya umarnin Ubangiji, to, Ubangiji zai yi gāba da ku. —1 Sama'ila 12.15a

Duk wanda bai zauna a cikina ba, za a yar da shi can, kamar reshe, yǎ bushe, a kuma tattara irinsu a jefa wuta, a ƙone. —Yahaya 15.6



## SANIN ALLAH, SAI DA NEMANSA

"Za ku neme ni ku same ni, idan kun neme ni da zuciya ɗaya." —Irmiya 29.13

Ka nema . . . kamar yadda za ka nemi . . . ɓoyayyiyar dukiya. Idan ka yi za ka . . . yi nasara a kan koyon sanin Allah. —Karin Magana 2.4b, 5

"Ku yi ta roƙo, za a ba ku. Ku yi ta nema, za ku samu. Ku yi ta ƙwanƙwasawa, za a kuwa buɗe muku." —Matiyu 7.7

In ba game da bangaskiya ba kuwa, ba shi yiwuwa a faranta masa rai. Domin duk wanda zai kusaci Allah, lalle ne ya gaskata, akwai shi, yana kuma sakamako ga masu nemansa. —Ibraniyawa 11.6

Ina ƙaunar waɗanda ke ƙaunata, dukan wanda ke nemana kuma zai same ni. —Karin Magana 8.17

Ubangiji mai alheri ne ga waɗanda suke sauraronsa, da wanda ke nemansa kuma. —Makoki 3.25

"Shi ne kuma ya halicci dukkan al'umma daga tsatso ɗaya, . . . wato nufinsa shi ne su neme shi, ko watakila sa laluba su same shi, alhali kuwa ba ya nesa da kowane ɗayanmu." —Ayyukan Manzanni 17.26a, 27

"In da ni ne kai, da sai in juya wurin Allah, in kai ƙarata a wurinsa." —Ayuba 5.8

## ALLAH YANA SO MU ZO WURINSA



"Gama Ubangiji Allahnku mai alheri ne, mai jinƙai, ba zai kawar da fuskarsa daga gare ku ba, idan kun komo gare shi." —2 Tarihi 30.9b

Ya Ubangiji, kai managarci ne, mai yin gafara, cike kake da madawwamiyar ƙauna ga dukan waɗanda suke yin addu'a gare ka. —Zabura 86.5

Ku kusaci Allah, shi ma zai kusace ku. —Yakubu 4.8a

Yana (Ubangiji) kusa da dukan waɗanda suke kira gare shi, waɗanda suke kiransa da zuciya ɗaya. —Zabura 145.18

Ubangiji ya ce, "Yanzu fa, bari mu daidaita al'amarinmu. Duk kun yi ja wur da zunubi, amma zan wanke ku, ku yi fari fat kamar auduga. Zai yiwu zunubinku ya sa ku zama ja wur, amma za ku yi fari fat kamar farin ulu." —Ishaya 1.18

Ku zo gare ni dukanku masu wahala, masu fama da kaya, ni kuwa zan hutasshe ku. Ku shiga bautata, ku kuma koya a gare ni, domin ni mai tawali'u ne, marar girmankai, za ku kuwa sami kwanciyar rai." —Matiyu 11.28, 29

Wanda kuwa ya zo gare ni ba zan kore shi ba ko kaɗan. —Yahaya 6.37b



## ALLAH MAI TSARKI NE

"Ya Ubangiji, . . . wa ke kamarka cikin ɗaukaka da tsarki?" —Fitowa 15.11a

"Babu wani mai tsarki kamar Ubangiji, babu wani mai kama da shi." —1 Sama'ila 2.2a

"Sam, Allah ba mai aikata mugunta ba ne, a wurin Mai Iko Dukka ba kuskure." —Ayuba 34.10b

"Mai Tsarki, Mai Tsarki, Mai Tsarki! Ubangiji Mai Runduna Mai Tsarki ne! Daukakarsa ta cika duniya." —Ishaya 6.3b

Gama haka wanda yake can Sama, Maɗaukaki, wanda ake kira Mai Tsarki ya ce, "Ina zaune a can Sama a tsattsarkan wuri." —Ishaya 57.15a

Ubangiji mai adalci ne a abin da yake yi duka, mai jinƙai ne a ayyukansa duka. —Zabura 145.17

"Ai, ba wani Managarci sai Allah kaɗai." —Markus 10.18b

"Wanene ba zai ji tsoronka ba, ya Ubangiji, ya kuma ɗaukaka sunanka? Domin kai kaɗai ne mai tsarki." —Wahayin Yahaya 15.4a

Ku yabi Ubangiji Allahnmu, ku yi sujada a bisa dutsensa mai tsarki! Ubangiji Allahnmu Mai Tsarki ne! —Zabura 99.9

"Mai tsarki, mai tsarki, mai tsarki, Ubangiji Allah Maɗaukaki, shi ne a dā, shi ne a yanzu, shi ne kuma nan gaba!" —Wahayin Yahaya 4.8b

## SAI MUTANEN ALLAH SU YI ZAMANSU DA TSARKI



Ka gaskata Allah ɗaya ne? To, madalla. Ai, ko aljannu ma sun gaskata, amma suna rawar jiki don tsoro. Kai marar azanci! Wato sai an nuna maka, bangaskiya ba tare da aikatawa ba, wofiya ce? —Yakubu 2.19, 20

Ta haka sai a ga waɗanda ke 'ya'yan Allah, da kuma waɗanda ke 'ya'yan Iblis, wato duk wanda ba ya aikata adalci, ba na Allah ba ne, haka kuma wanda ba ya ƙaunar ɗan'uwansa. —1 Yahaya 3.10

Ubangiji yana ƙin hanyoyin mugaye, amma yana ƙaunar mutumin da ke yin abin da ke daidai. —Karin Magana 15.9

Ku himmantu ga zaman lafiya da kowa, ku kuma zama a tsarkake, in banda shi kuwa, ba wanda zai ga Ubangiji. —Ibraniyawa 12.14

Amma da ya ke wanda ya kira ku mai tsarki ne, ku ma kanku sai ku zama tsarkaka cikin dukan al'amuranku. —1 Bitrus 1.15

Ku yi ƙoƙari, ku yi nagarta, ba mugunta ba, domin ku tsira. Sa'an nan ne Ubangiji Allah Maɗaukaki zai kasance tare da ku sosai, kamar yadda kuka ɗauka! —Amos 5.14

Abin da Ubangiji yake so gare ka, shi ne ka yi adalci, ka ƙaunaci aikata alheri, ka bi Allah da tawali'u. —Mika 6.8b

"Ku zama tsarkakakku, gama ni Ubangiji Allahnku mai tsarki ne." —Littafin Firistoci 19.2b

"Ka ƙaunaci Ubangiji Allahnka da dukkan zuciyarka, da dukkan ranka, da dukkan ƙarfinka, da dukkan hankalinka. Ka kuma ƙaunaci ɗan'uwanka kamar kanka." —Luka 10.27b

"Ka dai san umarnan nan, 'Kada ka yi kisankai. Kada ka yi zina. Kada ka yi sata. Kada ka yi shaidar zur. Kada ka yi zamba. Ka girmama mahaifinka da mahaifiyarka.' " —Markus 10.19

Kada ku biye wa zamanin nan, amma ku bar halinku ya sake ta wurin sabunta hankalinku ɗungum. —Romawa 12.2a

"Kada wannan littafin dokoki ya rabu da bakinka, amma zai zama abin da za ka yi ta tunani a kansa dare da rana domin ka kiyaye, ka kuma aikata bisa ga dukan abin da aka rubuta a ciki, gama ta haka za ka yi albarka cikin hanyarka, ta haka kuma za ka yi nasara." —Joshuwa 1.8

"Ku gaskata da Allah." —Markus 11.22b



Akwai abu shida, i, har bakwai ma, waɗanda Ubangiji ke ƙi, waɗanda ba zai haƙura da su ba, duban raini, harshe mai faɗar ƙarya, hannuwan da ke kashe marasa laifi, kwanyar da ke tunane-tunanen mugayen dabaru, mutum mai gaggawar aikata mugunta, mai yawan shaidar zur, mutum mai ta da fitina a tsakanin abokai. —Karin Magana 6.16-19

Ubangiji ya ce, "Ina ƙaunar aikin gaskiya, amma ina ƙin zalunci da aikata laifi." —Ishaya 61.8a

"Amma matsorata, da marasa amana, da masu aikin ƙyama, da masu kisankai, da fasikai, da masu sihiri, da masu bautar gumaka, da kuma duk maƙaryata, duk rabonsu tafkin nan ne mai cin wuta da kibritu, wanda yake shi ne mutuwa ta biyu." —Wahayin Yahaya 21.8

Domin haka ku kula fa, kada kowa ya ci amanar matarsa ta ƙuruciya. "Ni Ubangiji Mai Runduna, Allah na Isra'ila, na ce ina ƙin kisan aure." —Malakai 2.15b, 16a

"Kada ku ƙulla wa junanku sharri, kada kuma ku so yin rantsuwa ta ƙarya, gama ina ƙin waɗannan abubuwa duka, ni Ubangiji na faɗa." —Zakariya 8.17

Kana ƙaunar abin da ke daidai, kana ƙin abin da ke mugu. —Zabura 45.7a



"Amma fa na san ku, ba ku da ƙaunar Allah a zuci." —Yahaya 5.42

Duk wanda ke kiyaye dukkan Shari'a, amma ya saɓa kan abu guda, ya saɓi Shari'a gaba ɗaya ke nan. . . . Saboda haka duk wanda ya san abin da ya kamata, ya kuwa kasa yi, ya yi zunubi ke nan. —Yakubu 2.10; 4.17

Kamar yadda yake a rubuce cewa, "Babu wani mai adalci, babu, ko ɗaya." Gama 'yan adam duka sun yi zunubi, sun kasa kuma ga ɗaukakar Allah. —Romawa 3.10, 23

Duk wanda ba ya aikata adalci, ba na Allah ba ne, haka kuma wanda ba ya ƙaunar ɗan'uwansa. —1 Yahaya 3.10b

Dukanmu muna kama da tumakin da suka ɓata, kowannenmu ya kama hanyarsa. —Ishaya 53.6a

Sai na ce, "Sa zuciyata ya ƙare! Na shiga uku! Kowace maganar da ta fito bakina zunubi ce, ina zaune a tsakanin mutane waɗanda duk maganarsu zunubi ce, ba ta da tsarki. Amma yanzu da idona na ga Sarki, Ubangiji Mai Runduna!" —Ishaya 6.5

"Wa ya isa ya tsaya a gaban Ubangiji, Allahn nan mai tsarki?" —1 Sama'ila 6.20b



Na dai shaide su kan suna da himmar bauta wa Allah, amma ba da cikakken sani ba. Don saboda rashin fahimtar hanyar samun adalci wadda Allah ya tanadar, da kuma neman kafa tāsu hanya, sai suka ƙi bin ita wannan hanya ta samun adalci wadda Allah ya tanadar. —Romawa 10.2, 3

Dukanmu muka cika da zunubi har ayyukanmu mafi kyau ƙazamai ne duka. Saboda zunubanmu, muka zama kamar busassun ganyaye waɗanda iska take faucewa ta tafi da su. —Ishaya 64.6

"Idan na ce wa adali, ba shakka zai rayu, amma idan ya dogara ga adalcin da ya riga ya yi, sa'an nan ya shiga aikata laifi, ba za a tuna da ayyukan adalcinsa na dā ba. Zai mutu saboda laifin da ya yi." —Ezekiyel 33.13

Masu zaman halin mutuntaka, ba dama su faranta wa Allah rai. —Romawa 8.8

Ai, ba wani ɗan adam da zai sami kuɓuta ga Allah ta kiyaye ayyukan Shari'a. —Romawa 3.20a

Ba wai mun isar wa kanmu ba ne, har da za mu ce mu ne muke gudanar da wani abu, a'a, iyawarmu daga Allah take. —2 Korantiyawa 3.5



To, kamar yadda zunubi ya shigo duniya ta dalilin mutum ɗaya, zunubi kuwa shi ya jawo mutuwa, ta haka mutuwa ta zama gādo ga kowa, don kowa ya yi zunubi. —Romawa 5.12

Mugun buri kuma in ya yi ciki, yakan haifi zunubi. Zunubi kuma in ya balaga, yakan jawo mutuwa. —Yakubu 1.15

"Wanda ya yi zunubi shi zai mutu." —Ezekiyel 18.20a

Amma laifofinku suka raba tsakaninku da Allahnku. Zunubanku ne kuma suka sa ya juya daga gare ku don kada ya ji ku. —Ishaya 59.2

Mutumin da ya yi niyyar aikata abin da ke daidai zai rayu, amma mutumin da ya dukufa ga aikata mugunta zai mutu. —Karin Magana 11.19

"Ga abin da Allah ya ce, 'Don me kuke ƙetare umarnan Ubangiji, har da za ku rasa albarka? Saboda kun rabu da bin Ubangiji, shi ma ya rabu da ku.' " —2 Tarihi 24.20b

"Gama tayarwa kamar zunubin bokanci take. Taurinkai kuma kamar bautar gumaka yake. Kamar yadda ka ƙi umarnin Ubangiji, hakanan shi ma ya ƙi ka." —1 Sama'ila 15.23a



Allah alƙali ne mai adalci, kullum kuwa yana kā da mugaye. —Zabura 7.11

Ubangiji mai jinkirin fushi ne, Mai Iko Dukka. Ubangiji ba zai kuɓutar da mai laifi ba. —Nahum 1.3a

Saboda waɗannan abubuwa ne fushin Allah ke sauka kan kangararru. —Kolosiyawa 3.6

Gama ana bayyana fushin Allah daga Sama a kan dukan rashin bin Allah da aikin mugunta na mutanen da ke danne gaskiya ta aikin muguntarsu. —Romawa 1.18

Su masu aikata rashin adalci ne ƙwarai, da mugunta, da kwaɗayi, da ƙeta. Masu hassada ne, da kisankai, da jayayya, da ha'inci, da kuma nukura gaya matuƙa. Macizan ƙaiƙayi ne, da masu yanke, da maƙiyan Allah, da masu cin mutunci, da masu girmankai, da masu ruba, da masu haddasa mugunta, da marasa bin iyaye, da marasa fahimta, da masu ta da alkawari, da marasa ƙauna, da marasa tausayi. Waɗannan kuwa ko da ya ke sun san shari'ar Allah, cewa masu yin irin waɗannan abubuwa sun cancanci mutuwa, duk da haka ba aikata su kaɗai suke yi ba, har ma suna goyon bayan masu yinsu. —Romawa 1.29-32

## HUKUNCIN ALLAH YANA GABA

An ƙaddara wa ɗan adam ya mutu sau ɗaya ne, bayan haka kuma sai shari'a. —Ibraniyawa 9.27b

Sai na ga matattu manya da yara, tsaitsaye a gaban kursiyin, aka kuma buɗe littattafai. Sai kuma aka buɗe wani littafi, wanda yake shi ne Littafin Rai. Aka kuwa yi wa matattu shari'a bisa ga abin da ke rubuce cikin littattafan, gwargwadon aikin da suka yi. Duk wanda ba a sami sunansa a rubuce a Littafin Rai ba, sai a jefa shi a tafkin nan na wuta. —Wahayin Yahaya 20.12, 15

Abu ne fa mai matuƙar bantsoro a fāɗa cikin hukuncin Allah Rayayye. —Ibraniyawa 10.31

"Ina dai gaya muku, a Ranar Shari'a duk hululun da mutum ya yi, za a bincike shi." —Matiyu 12.36

Allah zai shara'anta kowane irin aiki, ko a ɓoye aka yi shi, ko nagari ne, ko mugu. —Mai Hadishi 12.14

"Haka zai kasance a ƙarshen duniya. Mala'iku za su fito, su ware mugaye daga masu adalci, su jefa su cikin wuta mai ruruwa. Nan za su yi kuka da cizon baki." —Matiyu 13.49, 50

Gama ya zo ne ya mallaki duniya. Zai mallaki dukan jama'ar duniya da adalci da gaskiya. —Zabura 96.13b

## BA DAMA MU ƁOYE DAGA WURIN ALLAH



Ubangiji yana ganin abin da ke faruwa a ko'ina, yana lura da mu, ko muna aikata alheri ko mugunta. —Karin Magana 15.3

Ya Ubangiji, ka jarraba ni, ka san ni. Ka san dukan abin da nake yi, tun daga can nesa ka gane dukan tunanina. Kana ganina, ko ina aiki, ko ina hutawa, ka san dukan ayyukana. Tun kafin in yi magana ka riga ka san abin da zan faɗa. —Zabura 139.1-4

"Gama yadda Ubangiji yake gani, ba haka mutum ke gani ba. Mutum yakan dubi kyan tsari ne kawai, amma Ubangiji yakan dubi zuciya." —1 Sama'ila 16.7b

Allah ya yi mana kunnuwa, shi ba zai ji ba? Allah ya yi mana idanu, shi ba zai gani ba? —Zabura 94.9

"Gama ina ganin dukan ayyukansu, ba a ɓoye suke a gare ni ba, muguntarsu kuma ba a ɓoye take a gare ni ba." —Irmiya 16.17

Ba wata halittar da za ta iya ɓuyar masa, amma kowane abu a fili yake, a shanye sosai a gaban idon wannan da yake da mu. —Ibraniyawa 4.13

"Gama yana ganin al'amuran mutum, yana kuma ganin dukan manufarsa. Ba wani duhu, ko duhu baƙi ƙirin inda masu aikata mugunta za su ɓuya." —Ayuba 34.21, 22



## ABIN DA AKE BUKATA SHI NE A JUYA DAGA ZUNUBI

"Ni Ubangiji Allah, na ce, ina jin daɗin mutuwar mugu ne? Ban fi so ya bar mugun halinsa ya rayu ba?" —Ezekiyel 18.23

"Ina gaya muku, ba haka ba ne! In kuwa ba ku tuba ba, duk za ku halaka kamarsu." —Luka 13.3

Ba za ka taɓa cin nasara a zamanka ba muddin kana ɓoye laifofinka. Ka hurta zunubanka ka tuba, sa'an nan Allah zai yi maka jinƙai. —Karin Magana 28.13

"Koyanzu," in ji Ubangiji, "Ku juyo wurina da zuciya ɗaya, da azumi, da kuka, da makoki, ku kyakkece zuciyarku, ba tufafinku kaɗai ba." Ku komo wurin Ubangiji Allahnku. Gama shi mai alheri ne, mai jinƙai, mai jinkirin fushi ne, mai yawan ƙauna. —Yowel 2.12, 13a

Ku komo wurin Ubangiji, ku roƙe shi, ku ce, "Ka gafarta mana zunubanmu, ka karɓe mu saboda alherinka." —Yusha'u 14.2a

"Zai raira waƙa a gaban jama'a, ya ce, 'Na yi zunubi. . . . Allah ya fanshe ni daga gangarawa zuwa kabari, raina kuwa zai ga haske.' " —Ayuba 33.27, 28

"Ku tuba, ku bar laifofinku domin kada su zama muku dalilin halaka." —Ezekiyel 18.30b

## TUBA TAKAN KAWO GAFARA



Ku juyo wurin Ubangiji, ku yi addu'a gare shi, yanzu da yake kusa. Bari mugaye su bar irin al'amuransu, su sāke irin tunaninsu. Bari su juyo wurin Ubangiji, Allahnmu, shi mai jinƙai ne, mai saurin gafartawa. —Ishaya 55.6, 7

Ubangiji yana kusa da waɗanda suka karai, yakan ceci waɗanda suka fid da zuciya. —Zabura 34.18

"Su bar mugayen ayyukansu don in gafarta musu . . . zunubinsu." —Irmiya 36.3b

Sa'an nan na hurta zunubaina gare ka, ban ɓoye laifofina ba. Na ƙudurta in hurta su gare ka, ka kuwa gafarta dukan laifofina. —Zabura 32.5

In kuwa muka bayyana zunubanmu, to, shi mai alkawari ne, mai adalci kuma, zai kuwa gafarta mana zunubanmu, ya tsarkake mu daga dukkan rashin adalci. —1 Yahaya 1.9

Saboda haka sai ku tuba, ku juyo, domin a shafe zunubanku. —Ayyukan Manzanni 3.19a

"Saboda haka sai ka tuba da wannan mugun aiki naka, ka roƙi Ubangiji ko a gafarta maka abin da ka riya a zuciyarka." —Ayyukan Manzanni 8.22

Tuba ita ce faɗar zunubanmu ga Allah, har da juyawa daga yin zunubi.



## SULHU DA ALLAH, SAI DA HADAYA

(Zunubi ya kawo rabuwa, shafi 14.)

Sai ya ɗibiya hannunsa a kan kan hadaya ta ƙonawar, za a karɓa masa, a kuwa yi masa gafara. Gama ran nama yana cikin jinin, Ubangiji kuwa ya ba su shi a bisa bagade domin a yi wa rayukansu kafara, gama da jini ake kafara saboda akwai rai a cikinsa. —Littafin Firistoci 1.4; 17.11

Hakika, bisa ga Shari'a, kusan kowane abu da jini ake tsarkake shi, in ba game da zubar da jini ba kuwa, ba gafara. —Ibraniyawa 9.22

"Tilas ne dabbar ta kasance lafiyayyiya ƙalau, bana ɗaya. Sa'an nan ku ɗibi jinin, ku sa a dogaran ƙofa duka biyu, da bisa kan ƙofar gidajen da za a ci naman dabbobin. Jinin da ke bisa gidajenku zai nuna inda kuke. Sa'ad da na ga jinin zan tsallake ku, ba kuma wani bala'in da zai same ku, ya hallaka ku." —Fitowa 12.5a, 7, 13a

Ibrahim ya ce, "Allah zai tanada wa kansa ragon hadayar ƙonawa, ya ɗana." Ibrahim ya ta da idanunsa, ya duba, ga rago kuwa a bayansa, da ƙahoni a sarƙafe cikin kurmi. Ibrahim kuwa ya tafi ya kamo ragon, ya miƙa shi hadayar ƙonawa maimakon ɗansa. —Farawa 22.8a, 13

## YESU SHI NE ƊAN RAGO WANDA ALLAH YA TANADA



. . . Yahaya ya tsinkayo Yesu na nufo shi, sai ya ce, "Kun ga, ga Ɗan Rago na Allah, mai ɗauke zunubin duniya!" —Yahaya 1.29

Aka ƙware shi ba tausayi, amma ya karɓa da tawali'u, bai ko ce uffan ba. Kamar ɗan rago wanda ake shirin yankawa, kamar tunkiya wadda ake shirin yi wa sausaya, bai ko ce uffan ba. —Ishaya 53.7

Almasihu ya shiga Wuri Mafi Tsarki sau ɗaya tak ba ƙari, ba kuwa ta jinin awaki ko na 'yan maruƙa ya shiga ba, sai dai ta nasa jini, ya samo mana madawwamiyar fansa. . . . Almasihu ma, . . . aka miƙa shi hadaya sau ɗaya tak, domin ya ɗauke zunuban mutane da yawa. —Ibraniyawa 9.12, 28a

Domin kun sani an fanshe ku ne . . . ba da abubuwa masu lalacewa ba kamar azurfa da zinariya, sai dai da jinin nan mai daraja na Almasihu, kamar na ɗan rago marar naƙasa, marar tabo. —1 Bitrus 1.18, 19

Balle fa jinin Almasihu wanda ya miƙa kansa marar aibu ga Allah, ta Madawwamin Ruhu, lalle zai tsarkake lamirinmu daga barin ibada marar tasiri, domin mu bauta wa Allah Rayayye. —Ibraniyawa 9.14

## BA FANSA, SAI TA WURIN HANYAR DA ALLAH YA SHIRYA

“Da ya ke mun sani mutum ba ya samun kuɓuta ga Allah ta wurin bin Shari'a, sai dai ta wurin gaskatawa da Yesu Almasihu kaɗai.” —Galatiyawa 2.16a

Domin ta wurin alheri ne aka cece ku saboda bangaskiya, wannan kuwa ba ƙoƙarin kanku ba ne, baiwa ce ta Allah. —Afisawa 2.8

Amma kuwa Allah na tabbatar mana da ƙaunar da yake mana, wato tun muna masu zunubi, Almasihu ya mutu dominmu. To, tun da ya ke yanzu an kuɓutar da mu ta jininsa, ashe kuwa, ta wurinsa za mu fi samun kārewa daga fushin Allah ke nan. Amma ta alherin da Allah ya yi musu kyauta sun sami kuɓuta ta wurin fansar da Almasihu Yesu ya yi. Allah kuwa ya ayyana Yesu Almasihu ya zama hadayar sulhu, ta wurin ba da gaskiya ga jininsa. —Romawa 5.8, 9; 3.24, 25a

“Shi ne duk annabawa suka yi wa shaida, cewa albarkacin sunansa duk mai gaskatawa da shi zai sami gafarar zunubai.” “Ba kuma samun ceto ga wani, domin ba wani suna duk duniyan nan da aka bayar cikin mutane, wanda lalle ta wurinsa ne za mu sami ceto.” —Ayyukan Manzanni 10.43; 4.12

## SHELAR HAIHUWAR YESU



A wata na shida Allah ya aiko mala'ika Jibra'ilu wani gari a ƙasar Galili, wai shi Nazarat, gun wata budurwa da aka ba da ta ga wani mutum mai suna Yusufu, na zuriyar Dawuda, sunan budurwar kuwa Maryamu. . . . Mala'ikan kuma ya ce mata,“Kada ki ji tsoro, Maryamu, kin sami tagomashi wurin Allah. Ga shi kuma, za ki yi ciki, ki haifi ɗa, ki kuma sa masa suna Yesu. Zai zama mai girma, za a kuma kira shi Ɗan Maɗaukaki. . . . Mulkinsa kuwa ba shi da matuƙa.” Sai Maryamu ta ce wa mala'ikan, “Ƙaƙa wannan zai yiwu, tun da ya ke ba a kai ni ɗaki ba?” Mala'ikan ya amsa mata ya ce, “Ruhu Mai Tsarki zai sauko miki, ikon Maɗaukaki kuma zai lulluɓe ki. Saboda haka Mai Tsarkin nan da za a haifa, za a kira shi Ɗan Allah. . . . Ba wata faɗar Allah da za ta kasa cika.” Sai Maryamu ta ce, “To, ga shi, ni baiwar Ubangiji ce, yă zamar mini yadda ka faɗa.” —Luka 1.26-38a

“Za ta haifi ɗa, za ka kuma sa masa suna Yesu, domin shi ne zai ceci mutanensa daga zunubansu.” —Matiyu 1.21

Mutum biyu kaɗai suka shigo duniya ba tare da gamuwar mace da namiji ba, su ne Adamu da Almasihu. Adamu ya kawo zunubi cikin duniya, amma Yesu ya kawo nasara bisa zunubi.



## YESU—DA GASKE SHI WANENE?

Wanda, ko da ya ke surar Allah yake, bai mai da daidaitakan nan tasa da Allah abar da zai riƙe kankan ce ba. Da ya bayyana da siffar mutum, sai ya ƙasƙantar da kansa ta yin biyayya, har wadda ta kai shi ga mutuwa, mutuwar ma ta gicciye. —Filibiyawa 2.6, 8

“Ni da Uba ɗaya muke.” “Kwa ce da wanda Uba ya keɓe, ya kuma aiko duniya, ‘Saɓo kake,’ domin na ce, ‘Ni Ɗan Allah ne’?” —Yahaya 10.30, 36

Yesu Almasihu, Kalma Madawwami, tun fil azal akwai shi. Ta wurin aikin al'ajabi Allah ya sa Maryamu ta ɗauki cikinsa. Ta wajen jiki an ce da shi Ɗan Mutum, ta wajen Ruhu kuwa an ce da shi Ɗan Allah. Littafi Mai Tsarki ya yi wannan magana “Ɗa” domin a nuna Allah da Kalmarsa, wato Yesu Almasihu.

Shi ya sa da Almasihu zai shigo duniya, sai ya ce, . . . “Amma kā tanadar mini jiki.” —Ibraniyawa 10.5

Amma ga tsarkinsa na ruhu shi Ɗan Allah ne, da iko aka ayyana shi haka ta wurin tashinsa daga matattu. —Romawa 1.4

Toma ya amsa masa ya ce, “Ya Ubangijina, Allahna kuma!” —Yahaya 20.28

YESU—DA GASKE SHI WANENE?



Ba shakka, asirin addininmu muhimmi ne ƙwarai, an bayyana shi da jiki. —1 Timoti 3.16a

Domin a cikinsa ne cikin jiki dukkan cikar allahntaka ke tabbata. —Kolosiyawa 2.9

Ga shi, an haifa mana ɗa! Mun sami yaro! Shi zai zama Mai Mulkinmu. Za a kira shi,“Mashawarci Mai Al'ajabi,” “Allah Maɗaukaki,” “Uba Madawwami,” “Sarkin Salama.” —Ishaya 9.6

Sai Yesu ya ce musu, . . . “Tun ba a haifi Ibrahim ba, ni ne.” —Yahaya 8.58

Shi ne tushen rai, wannan rai kuwa shi ne hasken mutane. Dā yana duniya, duniyar ma ta wurinsa ta kasance, duk da haka duniya ba ta san shi ba. —Yahaya 1.4, 10

Domin Allah ɗaya ne, matsakanci kuma ɗaya ne tsakanin Allah da mutane—Almasihu Yesu, mutum, wanda ya ba da kansa fansa saboda kowa da kowa. —1 Timoti 2.5, 6a

Wanda ta gare shi ne muka sami fansa, wato gafarar zunubanmu. Shi ne surar Allah marar ganuwa. —Kolosiyawa 1.14, 15a

Sai aka ji wata murya daga Sama ta ce, “Wannan shi ne Ɗana ƙaunataccena, wanda nake farin ciki da shi ƙwarai.” —Matiyu 3.17



## LITTAFI MAI TSARKI SHI NE MAGANAR ALLAH

Domin ba wani annabcin da ya taɓa samuwa ta nufin mutum, sai dai mutane ne Ruhu Mai Tsarki ke izawa, Allah na magana ta bakinsu. —2 Bitrus 1.21

“Yadda tuntuni ya faɗa ta bakunan annabawa nasa tsarkakan nan. Ka sanar da ceto ga jama'a tasa, wato ta samun gafarar zunubansu.” —Luka 1.70, 77

“Ruhun Ubangiji ya yi magana ta wurina, saƙonsa yana kan leɓunana.” —2 Sama'ila 23.2

“Waɗannan kalmomi da na umarce ku da su a yau, za su zauna a zuciyarku.” —Maimaitawar Shari'a 6.6

Kowane Nassi hurarre na Allah ne, mai amfani ne kuma wajen koyarwa, da tsawatarwa, da gyaran hali, da kuma tarbiyyar aikin adalci. —2 Timoti 3.16

Ai, duk abin da aka rubuta tun dā, an rubuta ne domin a koya mana, domin mu ɗore cikin sa zuciyan nan tamu ta haƙuri da ta'aziyyar da Littattafai ke yi mana. —Romawa 15.4

“Kun ɓāta ne, domin ba ku san Littattafai ba, ba ku kuma san ikon Allah ba.” —Matiyu 22.29b

Saboda ka nuna ɗaukakarka da umarnanka. —Zabura 138.2b

## YESU SHI NE KALMAR ALLAH



Yana saye da riga wadda aka tsoma a jini, sunan da ake kiransa da shi kuma, shi ne Kalmar Allah. —Wahayin Yahaya 19.13

Tun fil azal akwai Kalma, Kalman nan kuwa tare da Allah yake, Kalman nan kuwa Allah ne. Kalman nan kuwa ya zama mutum, ya zauna a cikinmu. —Yahaya 1.1, 14a

### Yesu ya Bayyana Allah

Domin shi Allah wanda ya ce, “Haske yă ɓullo daga duhu ya haskaka,” shi ne ya haskaka zukatanmu domin a haskaka mutane su san ɗaukakarsa a fuskar Yesu Almasihu. —2 Korantiyawa 4.6

Ba mutumin da ya taɓa ganin Allah daɗai. Makaɗaicin Ɗa, wanda yake yadda Allah yake, wanda kuma yake a wurin Uba, shi ne ya bayyana shi. —Yahaya 1.18

### Allah yana Magana ta wurin Yesu

A zamanin dā, Allah ya yi wa kakannin kakanninmu magana ta hanyoyi masu yawa iri iri, ta bakin annabawa, amma a zamanin nan na ƙarshe sai ya yi mana magana ta wurin Ɗansa, wanda ya sa magajin kome, wanda ta wurinsa ne kuma ya halicci duniya. —Ibraniyawa 1.1, 2

“Ina faɗar abin da na gani a wurin Ubana.” —Yahaya 8.38a

## MU KWATANTA MAGANAR ALLAH RUBUTACCIYA DA KALMAR ALLAH MAI RAI

### Littafi Mai Tsarki Abinci ne na Ruhu

Ɗanɗanon ka'idodinka akwai zaki, har sun fi zuma zaki.
—Zabura 119.103

“ ‘Ba da gurasa kaɗai mutum zai rayu ba, sai dai da kowace maganar da ke fitowa daga wurin Allah.’ ” —Matiyu 4.4b

### Littafi Mai Tsarki Haske ne a kan Hanyarmu

Maganarka fitila ce wadda za ta bi da ni, haske ne kuma a kan hanyata. Fassarar koyarwarka takan ba da haske, takan ba da hikima ga wanda bai ƙware ba.
—Zabura 119.105, 130

### Yesu Gurasa ne daga Sama

“Ni ne Gurasan rai da ya sauko daga Sama. Kowa ya ci Gurasan nan, zai rayu har abada. Har ma gurasar da zan bayar naman jikina ne, domin duniya ta rayu.” “Ni ne Gurasa mai ba da rai.”
—Yahaya 6.51, 48

### Yesu Hasken Duniya Ne

Shi ne tushen rai, wannan rai kuwa shi ne hasken mutane. Sai Yesu ya ƙara musu da cewa, “Ni ne Hasken duniya. Wanda ke bina ba zai yi tafiya a duhu ba, amma zai sami hasken rai.”
—Yahaya 1.4; 8.12



### Littafi Mai Tsarki yakan kawo Rai mai ba da Amfani

Maimakon haka, yana jin daɗin karanta shari'ar Allah, yana ta nazarinta dare da rana. Yana kama da itacen da ke a gefen ƙorama, yakan ba da 'ya'ya a kan kari, ganyayensa ba sa yin yaushi, yakan yi nasara a dukan abin da yake yi. —Zabura 1.2, 3

### Yesu yakan ba da Rai mai ba da Amfani

Ku zauna a cikina, ni kuma a cikinku. Ni ne itacen inabin, ku kuwa rassan. Wanda ya zauna a cikina, ni kuma a cikinsa, shi ne mai yin 'ya'ya da yawa. Domin in ba game da ni ba, ba za ku iya kome ba. —Yahaya 15.4a, 5

## LITTAFI MAI TSARKI YANA FAƊAR LABARIN YESU ALMASIHU

Kuna ta nazarin Littattafai, don a tsammaninku a cikinsu za ku sami rai madawwami, alhali kuwa su ne ke shaidata. Da dai kun gaskata Musa, da kun gaskata ni, domin labarina ya rubuta.
—Yahaya 5.39, 46

Sai ya fara ta kan littattafan Musa da na dukan annabawa, ya yi ta bayyana musu abubuwan da suka shafe shi a dukan Littattafai.
—Luka 24.27



## MAGANAR ALLAH MADAWWAMIYA BA TA SAKEWA

Maganarka tabbatacciya ce, ya Ubangiji, a kafe take a Sama. Cibiyar dokarka gaskiya ce, dukan ka'idodinka na adalci tabbatattu ne. —Zabura 119.89, 160

“Hakika ciyawa takan bushe, furanni kuwa su yi yaushi, amma maganar Allah ba za ta taɓa faɗuwa ba!” —Ishaya 40.8

“Kafin sararin sama da ƙasa su shuɗe, ko wasali ko ɗigo na Attaura ba za su shuɗe ba, sai an cika dukan kome.” —Matiyu 5.18b

“Nassi kuwa ba ya tashi.”
—Yahaya 10.35b

### Ba dama Mutum ya yi Karambani ya Sāke Maganar Allah

“Ku lura, ku aikata dukan abin da na umarce ku da shi, kada ku ƙara, kada ku rage daga cikinsa.”
—Maimaitawar Shari'a 12.32

“Kada ka yi ƙari a kan maganarsa, don kada ya tsauta maka, a kuma bayyana kai maƙaryaci ne.”
—Karin Magana 30.6

In kuma wani ya yi ragi a maganar littafin annabcin nan, Allah zai ɗauke rabonsa na itacen rai.
—Wahayin Yahaya 22.19a

Idan ka ƙi shawara mai kyau wahala kake nemar wa kanka.
—Karin Magana 13.13a



## MUTUWAR YESU TA CIKA SHIRIN ALLAH

“Domin wannan Uba ke ƙaunata, domin ina ba da raina in ɗauko shi kuma. Ba mai karɓe mini rai, don kaina nake ba da shi. Ina da ikon ba da shi, ina da ikon ɗauko shi kuma.” —Yahaya 10.17, 18a

Yesu ya amsa masa ya ce, “Ba ka da wani iko a kaina in ba an ba ka daga Sama ba.” —Yahaya 19.11a

“Kuna tsammani ba ni da ikon neman taimako gun Ubana, nan da nan kuwa ya aiko mini fiye da rundunar mala'iku goma sha biyu? To, ta yaya ke nan za a cika Littattafai kan lalle wannan abu ya kasance?” —Matiyu 26.53, 54

“Amma ta haka Allah ya cika faɗar da ya riga ya yi ta bakin annabawa duka, cewa Almasihunsa zai sha wuya.”
—Ayyukan Manzanni 3.18

“Shi Yesun nan fa, an ba da shi bisa ƙaddarar Allah da rigyasaninsa, ku kuwa kuka gicciye shi, kuka kashe shi, ta hannun masu zunubi.” —Ayyukan Manzanni 2.23

Ubangiji ya ce, “Nufina ne ya sha wahala, mutuwar kuwa hadaya ce domin ta kawo gafara.”
—Ishaya 53.10a

Shi da bai hana Ɗansa ba, sai ma ya ba da shi saboda mu duka, ashe, ba zai ba mu kome tare da shi hannu sake ba? —Romawa 8.32



## SHAIDU SUN FAƊI LABARIN MUTUWAR YESU

Suka kuma gicciye 'yan fashi biyu tare da shi, ɗaya dama da shi, ɗaya kuma a hagun. Wannan shi ne cikar Nassin nan da ya ce, “An lasafta shi a cikin masu laifi.”
—Markus 15.27, 28

To, tun daga tsakar rana, duhu ya rufe ƙasa duka, har zuwa ƙarfe uku na yamma. . . . Sai Yesu ya sāke ɗaga murya da ƙarfi, sa'an nan ya sāki ransa. . . . Ƙasa ta yi girgiza, duwatsu kuma suka tsattsage. Sa'ad da jarumin da waɗanda ke tare da shi suna tsaron Yesu suka ga rawar ƙasa da kuma abin da ya auku, sai duk tsoro ya kama su, suka ce, “Hakika wannan Ɗan Allah ne!” —Matiyu 27.45, 50-51b, 54

Sai soja suka zo suka karya ƙafafun na farkon nan, da kuma na ɗayan da aka gicciye tare da shi. Amma da suka zo wurin Yesu, suka kuma ga ya riga ya mutu, ba su karya ƙafafunsa ba. Sai dai ɗaya daga cikin sojan nan ya soke shi da mashi a kwiɓi, nan da nan ga jini da ruwa suka gudano. Wanda ya gani ɗin kuwa ya ba da shaida kan haka, shaida tasa kuwa gaskiya ce, ya kuma san gaskiya yake faɗa, domin ku ma ku ba da gaskiya. Wannan kuwa don a cika Nassi ne cewa, “Kashinsa ɗaya ba za a karya ba.” Wani Nassi kuma ya ce, “Za su dubi wanda suka soka.” —Yahaya 19.32-37



## YESU YA CI NASARA BISA MUTUWA

“Amma Allah ya tashe shi bayan ya ɓalle masa ƙangin mutuwa, domin ba shi yiwuwa mutuwa ta riƙe shi. Yesun nan kam, Allah ya tashe shi daga matattu, mu kuwa duk shaidu ne ga haka.”
—Ayyukan Manzanni 2.24, 32

Wato tun da ya ke 'ya'yan duk suna da tsoka da jini, shi ma sai ya ɗauki kamannin haka, domin ya hallakar da mai ikon mutuwa, wato Iblis, ta mutuwarsa, yă kuma 'yanta duk waɗanda tun haihuwarsu suke zaman bauta saboda tsoron mutuwa.
—Ibraniyawa 2.14, 15

“Ke mutuwa, ina nasararki? Ke mutuwa, ina ƙarinki?” Godiya tā tabbata ga Allah wanda ke ba mu nasara ta wurin Ubangijinmu Yesu Almasihu.
—1 Korantiyawa 15.55, 57

“Ni ne kuma Rayayye. Dā na mutu, amma ga shi yanzu, ina raye har abada abadin, ina kuwa da mabuɗan mutuwa da na Hades.”
—Wahayin Yahaya 1.18

Wadda yanzu aka bayyana, ta bayyanar Mai Cetonmu Almasihu Yesu, wanda ya shafe mutuwa, ya kuma bayyana rai da rashin mutuwa, ta bishara. —2 Timoti 1.10

Amma ga hakika an ta da Almasihu daga matattu, shi ne ma nunan fari na waɗanda suka yi barci. —1 Korantiyawa 15.20

## MU DAI, ME ZA MU YI DA YESU?

“Ga ni nan tsaye a bakin ƙofa, ina ƙwanƙwasawa, kowa ya ji muryata ya buɗe ƙofar, sai in shiga wurinsa, in ci abinci tare da shi, shi kuma tare da ni.”
—Wahayin Yahaya 3.20

Wanda ba ya aikin lada, amma yana sa dogararsa ga Allah wanda ke kuɓutar da masu laifi, a kan lasafta bangaskiyan nan tasa adalci ce. —Romawa 4.5

“Ku karɓi Ruhu Mai Tsarki.” . . . “Ku roƙa, za ku samu, domin farin cikinku ya zama cikakke.”
—Yahaya 20.22b; 16.24b

Wato in kai da bakinka ka bayyana yarda, cewa Yesu Ubangiji ne, ka kuma gaskata a zuciyarka Allah ya tashe shi daga matattu, za ka sami ceto. —Romawa 10.9

“Wanda duk ya fi son ubansa ko uwarsa fiye da ni, bai cancanci zama nawa ba.” . . . Sai Yesu ya ce wa almajiransa, “Duk mai son bina, sai ya ƙi kansa, ya ɗauki gicciyensa, ya bi ni. Duk mai son tattalin ransa, zai rasa shi. Duk kuwa wanda ya rasa ransa saboda ni, zai same shi.”
—Matiyu 10.37a; 16.24, 25

In kuwa ku na Almasihu ne, ashe, ku zuriyar Ibrahim ne, magāda ne kuma bisa ga alkawarin nan. —Galatiyawa 3.29

## TA WURIN YESU MUNA DA SABON RAI



Allah yā ba mu rai madawwami, wannan rai kuwa yana cikin Ɗansa. Duk wanda ke da Ɗan, yana da rai.Wanda ba shi da Ɗan Allah kuwa, ba shi da rai.
—1 Yahaya 5.11b, 12

Amma Allah da ya ke mai yalwar jinƙai ne, . . . ko a sa’ad da muke matattu ma ta wurin laifofinmu, sai ya rayar da mu tare da Almasihu. —Afisawa 2.4a, 5a

“An gicciye ni tare da Almasihu. Yanzu ba ni ne kuma ke raye ba, Almasihu ne ke raye a cikina. Rayuwan nan kuma da nake yi ta jiki, rayuwa ce ta wurin bangaskiya ga Ɗan Allah.”
—Galatiyawa 2.20a

Ka’idan nan ta Ruhu mai ba da rai da ke ga Almasihu Yesu ta ’yanta ni daga ka’idar zunubi da ta mutuwa. —Romawa 8.2

Saboda haka, duk wanda ke na Almasihu, sabuwar halitta ne, tsohon al’amari duk ya shuɗe, ga shi, kome ya zama sabo.
—2 Korantiyawa 5.17

Gama sāke haifarku aka yi, ba ta iri mai lalacewa ba, sai dai marar lalacewa, wato ta Maganar Allah rayayyiya, dawwamammiya. . . . Kamar jariri sabon haihuwa, ku yi marmarin shan madara marar gami mai ruhu, domin ku girma da shi, har ya kai ku ga samun ceto. —1 Bitrus 1.23; 2.2



## ALLAH UBA NE GA MUTANENSA

Allah, wanda yake zaune a tsattsarkan Haikalinsa, yana lura da marayu, yana kuwa kiyaye gwauraye, wato matan da mazansu suka mutu. —Zabura 68.5

Amma kai ne Ubanmu, ya Ubangiji. Mu kamar yumɓu ne, kai kuwa kamar maginin tukwane. Kai ka halicce mu. Ya Ubangiji, kai ne Ubanmu. Kai ne Mai Fansarmu a koyaushe.
—Ishaya 64.8; 63.16b

“Maimakon kuma a ce, ‘Ku ba mutanena ba ne,’ za a ce, ‘Ku mutanen Allah ne mai rai.’ ”
—Yusha’u 1.10b

“To, ku da kuke mugaye ma, kuka san yadda za ku ba ’ya’yanku kyautar kyawawan abubuwa, balle Ubanku na Sama da zai ba da abubuwan alheri ga masu roƙonsa?” . . . “Saboda haka sai ku yi addu’a kamar haka, ‘Ya Ubanmu wanda ke cikin Sama, a kiyaye sunanka da tsarki.”
—Matiyu 7.11; 6.9

“Ni kuwa in yi na’am da ku, in kasance Uba gare ku, ku kuma ku kasance ’ya’yana, mata da maza, in ji Ubangiji Maɗaukaki.”
—2 Korantiyawa 6.17b, 18

Duk waɗanda Ruhun Allah ke bishe su, su ne ’ya’yan Allah.
—Romawa 8.14

## TA WURIN YESU MUN SANI ALLAH UBANMU NE



Yesu ya ce masa, “Ni ne hanya, ni ne gaskiya, ni ne kuma rai. Ba mai zuwa wurin Uba sai ta wurina. Da kun san ni, da kun san Ubana ma. Amma daga yanzu kun san shi, kun kuma gan shi.” “Kowa ke ƙaunata, zai kiyaye maganata, Ubana kuwa zai ƙaunace shi, za mu zo wurinsa mu zauna tare da shi.” —Yahaya 14.6, 7, 23b

Allah ya aiko Ɗansa, . . . domin ya . . . mai da mu a matsayin ’ya’yan Allah. Tun da ya ke ku ’ya’ya ne, sai Allah ya aiko Ruhun Ɗansa cikin zukatanmu, yana kira, “Ya Abba! Uba!” Don haka, kai ba bawa ba ne kuma, ɗa ne. Da ya ke ɗa ne kuma, to, magaji ne bisa ga ikon Allah. Domin dukanku ’ya’yan Allah ne, ta wurin bangaskiya ga Almasihu Yesu.
—Galatiyawa 4.4b-7; 3.26

Amma duk iyakar waɗanda suka karɓe shi, wato masu gaskatawa da sunansa, ya ba su ikon zama ’ya’yan Allah. —Yahaya 1.12

In kuwa wani ya yi zunubi, muna da Mai Taimako a gun Uba, wato Yesu Almasihu mai adalci.
—1 Yahaya 2.1b

Domin ta gare shi ne dukanmu biyu muka sami isa gun Uba ta hanyar Ruhu guda. —Afisawa 2.18



## YESU YAKAN KAWO MANA KAUNA, DA MURNA, DA SALAMA

Allah shi ne ƙauna, wanda ke a dawwame cikin ƙauna kuwa, ya dawwama a cikin Allah ke nan, Allah kuma a cikinsa.
—1 Yahaya 4.16b

Ku yi wa juna kirki, kuna tausayi, kuna yafe wa juna kamar yadda Allah ya yafe muku ta wurin Almasihu. —Afisawa 4.32

“Ta haka kowa zai gane ku almajiraina ne, in dai kuna ƙaunar juna.” —Yahaya 13.35

Albarkar Ruhu kuwa ita ce ƙauna, da farin ciki, da salama.
—Galatiyawa 5.22a

Za ka nuna mini hanyar rai, kasancewarka takan sa in cika da farin ciki, taimakonka kuwa yana kawo jin daɗi har abada.
—Zabura 16.11

Duk da haka zan yi farin ciki da Ubangiji, zan yi murna da Allah Mai Cetona. —Habakuk 3.18

To, da ya ke mu kuɓutattu ne ta wurin bangaskiya, muna da salama ke nan a gun Allah ta wurin Ubangijinmu Yesu Almasihu.
—Romawa 5.1

“Na bar ku da salama. Salamata nake ba ku. Ba kamar yadda duniya ke bayarwa nake ba ku ba. Kada ku damu, kada kuma ku ji tsoro.” —Yahaya 14.27

## YESU ZAI TA DA MASU BINSA NA GASKIYA DAGA CIKIN MATATTU



In kuwa Ruhun wannan da ya ta da Yesu daga matattu na zaune a zuciyarku, to, shi da ya ta da Almasihu Yesu daga matattu zai kuma raya jikin nan naku mai mutuwa, ta Ruhunsa da ke zaune a zuciyarku. —Romawa 8.11

Allah ya ta da Ubangiji daga matattu, haka mu ma zai ta da mu da ikonsa. —1 Korantiyawa 6.14

“Gama nufin Ubana, shi ne duk wanda ke duban Ɗan, yake kuma gaskatawa da shi, yǎ sami rai madawwami, ni kuma zan tashe shi a ranar ƙarshe.” —Yahaya 6.40

Yesu ya ce mata, “Ai, ni ne tashin matattu, ni ne kuma rai. Wanda ya gaskata da ni, ko ya mutu zai rayu. Wanda kuwa ke raye, yake kuma gaskatawa da ni, ba zai mutu ba har abada.”
—Yahaya 11.25, 26a

Tun da ya ke mutuwa ta wurin mutum ta faru, haka kuma tashin matattu ta wurin Mutum yake. Kamar yadda duk ake mutuwa saboda Adamu, haka duk za a rayar da kowa saboda Almasihu. Amma kowanne bi da bi, Almasihu ne nunan fari, sa’an nan a ranar komowa tasa, waɗanda ke na Almasihu. —1 Korantiyawa 15.21-23

“Saboda ni a raye nake, ku ma za ku rayu.” —Yahaya 14.19b

## 40 KADA KA ƘYALE WANNAN CETO MAI GIRMA

Kowa ya yar da Shari'ar Musa, a kan kashe shi ba tausayi, a kan shaidu biyu ko uku. To, mutumin da ya raina Ɗan Allah, ya kuma tozarta jinin nan na tabbatar alkawari, wanda aka tsarkake shi da shi, har ya wulakanta Ruhun alheri, wane irin hukunci mafi tsanani kuke tsammani ya cancanta fiye da wancan?
—Ibraniyawa 10.28, 29

"Wanda ya ƙi ni, bai kuma karɓi maganata ba, yana da mai hukunta shi, maganar da na faɗa, ita za ta hukunta shi a ranar ƙarshe."
—Yahaya 12.48

"Shi ya sa na ce muku za ku mutu da zunubanku. Domin in ba ku gaskata ni ne shi ba, za ku mutu da zunubanku." —Yahaya 8.24

"Ya ku masoyana, ina dai gaya muku, kada ku ji tsoron masu kisan mutum, bayan sun kashe kuwa, ba abin da za su iya yi. Amma zan gaya muku wanda za ku ji tsoro. Ku ji tsoron wannan da in ya kashe, yana da ikon jefawa Gidan Wuta. Hakika, ina gaya muku, shi za ku tsorata!" —Luka 12.4, 5

Ta ƙaƙa mu za mu tsira, in mun ƙi kula da babban ceto haka?
—Ibraniyawa 2.3a

"Wanda ya ƙi bin Ɗan kuwa, ba zai sami rai ba, sai dai fushin Allah ya tabbata a gare shi."
—Yahaya 3.36b

## YESU ALMASIHU ZAI YI MANA HUKUNCI 41

"Tun da ya ke ya tsai da ranar da zai yi wa duniya shari'a, shari'ar adalci, ta wurin mutumin nan da ya sa, wannan kuwa ya tabbatar wa dukan mutane, da ya tashe shi daga matattu."
—Ayyukan Manzanni 17.31

"Uba ba ya hukunta kowa, sai dai yā danƙa dukkan hukunci ga Ɗan, domin kowa yă girmama Ɗan, kamar yadda ake girmama Uban." —Yahaya 5.22, 23a

Don lalle ne a gabatar da mu duka a gaban gadon shari'a na Almasihu, domin kowa ya sami sakamakon abin da ya yi . . . ko mai kyau ko marar kyau.
—2 Korantiyawa 5.10

A wannan rana Allah zai yi wa 'yan adam shari'a a kan asiransu, ta wurin Yesu Almasihu.
—Romawa 2.16a

A ranar bayyanar Ubangiji Yesu daga Sama tare da manyan mala'ikunsa, a cikin wuta mai ruruwa, yana ta saka wa waɗanda suka ƙi sanin Allah, da kuma waɗanda suka ƙi bin bisharar Ubangijinmu Yesu. Za su sha hukuncin madawwamiyar halaka, suna ware da zatin Ubangiji.
—2 Tasalonikawa 1.7b-9a

" 'Waɗannan maƙiya nawa kuwa da ba sa so in yi mulki a kansu, ku kawo su nan a kashe su a gabana.' " —Luka 19.27

## 42 BA DUKKAN MASU CEWA SUN BI YESU, NA YESU NE NA GASKIYA

Suna cewa sun san Allah, amma suna saɓa masa ta aikinsu.
—Titus 1.16a

Duk wanda ba shi da Ruhun Almasihu kuwa, ba na Almasihu ba ne. —Romawa 8.9b

Sukan zo wurinka su zauna, sai ka ce su mutanena ne, sukan ji abin da ka ce, amma ba za su aikata ba, gama suna nuna ƙauna da baka, amma sun ƙwallafa zuciyarsu a kan ƙazamar riba.
—Ezekiyel 33.31

" 'Al'umman nan a baka kawai suke girmama ni, amma a zuci nesa suke da ni.' " —Matiyu 15.8

"Ba duk mai ce mini, 'Ya Ubangiji, ya Ubangiji,' ne zai shiga Mulkin Sama ba, sai dai wanda ya yi abin da Ubana da ke cikin Sama ke so. A ranan nan da yawa za su ce mini, 'Ya Ubangiji, ya Ubangiji, ashe, ba mu yi annabci da sunanka ba? Ba mu fitar da aljannu da sunanka ba? Ba mu kuma yi ayyukan al'ajabi masu yawa da sunanka ba?' Sa'an nan zan ce musu, 'Ni ban taɓa saninku ba. Ku rabu da ni, ku masu yin mugun aiki.' " —Matiyu 7.21-23

Hakanan a idon mutane ku adalai ne, amma ciki sai munafunci da mugun aiki. —Matiyu 23.28

## MASU BIN YESU NA GASKIYA SUNA MASA BIYAYYA 43

Ta haka za mu tabbata mun san shi, in dai muna bin umarninsa.
—1 Yahaya 2.3

Zan sa ruhuna a cikinku, in sa ku bi dokokina, ku kiyaye ka'idodina. —Ezekiyel 36.27

Da ya kai ga kammala, sai ya zama tushen madawwamin ceto ga dukkan waɗanda suke masa biyayya. —Ibraniyawa 5.9

Da aka 'yanta ku kuma daga bautar zunubi, kun zama bayin aikin adalci. —Romawa 6.18

Ai, mu aikinsa ne, an sāke halittarmu cikin Almasihu Yesu musamman domin mu yi kyawawan ayyuka, waɗanda Allah ya tanadar mana tun da fari, mu yi.
—Afisawa 2.10

In kuwa Almasihu na zuciyarku, ba ruwan jikinku da zunubi ke nan, Ruhu kuwa rai ne a gare ku saboda kun sami adalcin Allah. In kuna zaman halin mutuntaka, za ku mutu ke nan, amma in da ikon Ruhu kuka kashe ayyukan nan na halin mutuntaka, sai ku rayu.
—Romawa 8.10, 13

"Duk wanda ya bayyana yarda ga sunan Ubangiji, to, yă yi nesa da aikata mugunta."
—2 Timoti 2.19b

## 44 MUTANEN DUNIYA SUNA ƘIN MASU BIN YESU

"In duniya ta ƙi ku, ku sani sai da ta ƙi ni kafin ta ƙi ku. Da ku na duniya ne da duniya ta so abinta, amma saboda ku ba na duniya ba ne, na kuma zaɓe ku daga duniya, shi ya sa duniya take ƙinku."
—Yahaya 15.18, 19

"Hakika, lokaci ma na zuwa da kowa ya kashe ku zai zaci bautar Allah yake yi. Za su yi haka ne kuwa domin ba su san Uba ko ni ba." —Yahaya 16.2b, 3

Ku dubi irin ƙaunar da Uba ya nuna mana, har yake ce da mu 'ya'yan Allah, haka kuwa muke. Abin da ya sa duniya ba ta san mu ba, don ba ta san shi ba ne.
—1 Yahaya 3.1

Sai da shan wuya mai yawa za mu shiga Mulkin Allah.
—Ayyukan Manzanni 14.22b

Labudda duk masu niyyar zaman tsarkaka, suna na Almasihu Yesu, za su sha tsanani.
—2 Timoti 3.12

"A duniya kuna shan wuya, amma dai ku yi farin ciki, ai, na yi nasara da duniya." —Yahaya 16.33b

"Albarka tā tabbata gare ku sa'ad da mutane suka ƙi ku, suka kuma ware ku, suka zage ku, suka yi ƙyamar sunanku saboda Ɗan Mutum." —Luka 6.22

## ALKAWARAI GA WAƊANDA SUKE SHAN TSANANI 45

Ku jibga masa dukan taraddadinku, domin yana kula da ku.
—1 Bitrus 5.7

"Kada ka ji tsoro, ina tare da kai, ni ne Allahnka, kada ka bar kome ya firgita ka. Zan sa ka yi ƙarfi, in kuma taimake ka, zan kiyaye ka, in cece ka. —Ishaya 41.10

Mai yiwuwa ne ubana da uwata su yashe ni, amma Ubangiji zai lura da ni. —Zabura 27.10

Saboda haka ma iya fitowa gabagaɗi, mu ce, "Ubangiji shi ne mataimakina, ba zan ji tsoro ba. Me mutum zai iya yi mini?"
—Ibraniyawa 13.6

Albarka ta tabbata a gare ku in ana zaginku saboda sunan Almasihu, don Ruhun ɗaukaka, wato Ruhun Allah yā tabbata a gare ku. —1 Bitrus 4.14

Allah zai sa mala'ikunsa su lura da kai, za su kiyaye ka duk inda za ka tafi. Ko da hanyan nan ta bi ta tsakiyar duhu na mutuwa, ba zan ji tsoro ba, ya Ubangiji, gama kana tare da ni! —Zabura 91.11; 23.4a

Zan iya yin kome albarkacin wannan da yake ƙarfafata. Allahna kuma zai biya muku kowace bukatarku daga cikin yalwar ɗaukakarsa da ke ga Almasihu Yesu.
—Filibiyawa 4.13, 19

## NASARA A KAN ZUNUBI DA SHAIƊAN

Ba wani gwajin da ya taɓa samunku, wanda ba a saba yi wa ɗan adam ba. Allah mai alkawari ne, ba zai kuwa yarda a gwada ku fin ƙarfinku ba, amma game da gwajin sai ya ba da mafita, yadda za ku iya jure shi.
—1 Korantiyawa 10.13

Saboda haka sai mu kusaci kursiyin Allah na alheri da amincewa, domin a yi mana jinƙai, a kuma yi mana alherin da zai taimake mu a kan kari. —Ibraniyawa 4.16

Don haka sai ka guje wa mugayen sha'awace-sha'awacen ƙuruciya, ka dimanci aikin adalci, da bangaskiya, da ƙauna, da kuma salama. —2 Timoti 2.22a

In kuwa muna zaune a haske kamar yadda shi yake cikin haske, muna tarayya da juna ke nan, jinin Yesu Ɗansa kuma yana tsarkake mu daga dukkan zunubi.
—1 Yahaya 1.7

Haka ku ma sai ku lasafta kanku kamar ku matattu ne ga zunubi, amma kuna raye, rayuwa ga Allah, ta Almasihu Yesu.
—Romawa 6.11

Saboda haka ku miƙa kanku ga Allah, ku yi tsayayya da Iblis, lalle kuwa zai guje muku.
—Yakubu 4.7

Na riƙe maganarka a zuciyata, don kada in yi maka zunubi.
—Zabura 119.11

## ADDU'A TA GASKIYA ITA CE ZUMUNTA DA ALLAH



Ka ce, "Zo wurina," zan kuwa zo gare ka, ya Ubangiji.
—Zabura 27.8

Ya jama'ata, ku dogara ga Allah a kowane lokaci! Ku faɗa masa dukan wahalarku, gama shi ne mafakarmu. —Zabura 62.8

Ubangiji, ka warkar da ni, zan kuwa warke, ka cece ni, zan kuwa cetu, gama kai ne abin yabona.
—Irmiya 17.14

Ku riƙa yin addu'a ba fasawa. Ku yi godiya ga Allah a kowane hali, domin shi ne nufin Allah game da ku ta wurin Almasihu Yesu. —1 Tasalonikawa 5.17, 18

In waninku ya rasa hikima, sai ya roƙi Allah, mai ba kowa hannu sake, ba tare da gori ba, sai kuwa a ba shi. —Yakubu 1.5

"In kun zauna a cikina, maganata kuma ta zauna a cikinku, za ku roƙi duk abin da kuke so, za a kuwa yi muku." —Yahaya 15.7

Na yi addu'a ga Ubangiji, ya kuwa amsa mini, ya kuɓutar da ni daga dukan tsorona. —Zabura 34.4

Da ban watsar da zunubaina ba, da Ubangiji bai ji ni ba. Ka cika alkawarinka, ya Ubangiji, ka gafarta zunubaina, gama suna da yawa.
—Zabura 66.18; 25.11



## YESU YANA ZUWA—KA YI SHIRI!

Domin Ubangiji kansa ma zai sauko daga Sama da kira mai ƙarfi, da muryar babban mala'ika, da kuma busar ƙahon Allah. Waɗanda suka mutu suna na Almasihu, su ne za su fara tashi, sa'an nan sai mu da muka wanzu, muke raye, za a ɗauke mu tare da su ta cikin gajimare, mu sadu da Ubangiji a sararin sama, sai kuma kullum mu kasance tare da Ubangiji.
—1 Tasalonikawa 4.16, 17

Ya ku ƙaunatattu, tun da aka yi mana waɗannan alkawarai, sai mu tsarkake kanmu daga kowace irin ƙazanta ta jiki ko ta zuci, da bangirma ga Allah mu kamalta cikin tsarki. —2 Korantiyawa 7.1

To yanzu, ya ku 'ya'yana ƙanana, sai ku zauna cikinsa, domin sa'ad da ya bayyana, mu kasance da amincewa, kada kunya ta rufe mu a gabansa a ranar komowa tasa. —1 Yahaya 2.28

Ku ma sai ku yi haƙuri, ku tsai da zukatanku, domin ranar komowar Ubangiji ta yi kusa. 'Yan'uwa, kada ku yi wa juna gunaguni, don kada a hukunta ku. Ga mai shari'a a bakin ƙofa!
—Yakubu 5.8, 9

"Ku ma sai ku zauna a kan shiri, domin a lokacin da ba ku zata ba Ɗan Mutum zai zo."
—Luka 12.40

## KA CIKA DA RUHUN ALLAH

Ku kasa kunne lokacin da nake tsauta muku, zan ba ku shawara mai kyau, mu yi tarayya cikin ilimina. —Karin Magana 1.23

"Sai ku tuba, a yi wa kowannenku baftisma, kan kun yarda da sunan Yesu Almasihu, domin a gafarta zunubanku, za ku kuwa sami baiwar Ruhu Mai Tsarki." —Ayyukan Manzanni 2.38b

Kada kuma ku bugu da giya, hanyar masha'a ke nan. Sai dai ku cika da Ruhu, kuna zance da junanku da kalmomin zabura, da waƙoƙin yabo, da waƙoƙi na ruhu, kuna raira waƙoƙi da zabura ga Ubangiji da yabo a zukatanku. Kullum ku riƙa gode wa Allah Uba da sunan Ubangijinmu Yesu Almasihu a kan komenene. Ku bi juna saboda ganin girman Almasihu.
—Afisawa 5.18-21

Domin Allah shi ne mai aiki a zukatanku ku nufi abin da ke kyakkyawan nufinsa, ku kuma aikata shi. —Filibiyawa 2.13

Ashe, ba ku sani ku haikalin Allah ne ba, Ruhun Allah kuma na zaune a zuciyarku? Sayenku aka yi da tamani. To, sai ku ɗaukaka Allah da jikinku.
—1 Korantiyawa 3.16; 6.20

If you are interested in receiving additional studies of God's Word, write to the publisher in English:

**W. M. Press, Inc.**
**P.O. Box 120**
**New Paris, IN 46553-0120 USA**

Kyauta—Kada a sayar

www.wmpress.org

Hausa HKG